# Mutane Uku Allah baya Magana da su, kuma bazai tsarkake su ba kuma suna da Aaba Mai Radadi " Tsohon Mazinaci da Talaka Mai girman Kai, da Mutumin da ya maida Allah Hajarsa bazai iya siya ba sai yayi rantsuwa kuma bazai iya siyarwa ba sai yayi Rantsuwa.

Daga Salaman Alfarisi - Allah ya yarda da shi- daga Annabi "Mutane Uku Allah baya Magana da su, kuma bazai tsarkake su ba kuma suna da Aaba Mai Radadi " Tsohon Mazinaci da Talaka Mai girman Kai, da Mutumin da ya maida Allah Hajarsa bazai iya siya ba sai yayi rantsuwa kuma bazai iya siyarwa ba sai yayi Rantsuwa."
[Ingantacce ne] [Al-Tabrani Ya Rawaito shi]

Annabi yana bamu labarin wasu Kala uku na masu Sabo, wadan daza'a yi musu Ukuba mafi Tsanani; sabida Munin abunda suka aikata Na farkosu: Wanda ya aikata zina bayan ya girma, domin dalilan sabo a gareshi sun raunana a halin da yake, sai ya nuna cewa dalilin yin sabonsa ba komai bane sai son Alfasha da Fajirci, koda ya kasance Zina dai Abun ki ce ga kowa to tasa ita mafi Muni Na biyu: Talaka Mai girman Kai ga Mutanekuma Girman kai abun ki ne ga kowa amma ga Talaka ne da bashi da komai da zai sa shi girman mafi muni domin girman kansa a halin bashi da abunda zai janyo masa girman kan wannan ya nuna cewa wannan mummunar dabi'ar a halinsa ne Na uku: kuma duk wanda ya sanya Allah abin wasansa da rantsuwa kamar wata hajarsa, kuma yana yawan amfani da ita a siye da sayarwarsa sai ya rika wulakanta sunan Allah kuma ya sanya shi hanyar neman kudinsa.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5952